# Sairri da Kai

Mahalarta taron za su bincika wane irin bayani ne za a iya ajiyewa cikin “sirri” da kyau, yanda ake tsara saitunan sirri a kan dandalin sadarwar zamani, da yanda za a yi bayani a kan shirinsu na yanke shawara a kan sirrinsu (misali., me yasa a ka saita wani abun zuwa “abokai kawai” da saitin “kowa da kowa”).

## Kayayyaki darasi

Takardar Darasi a kan Wasan Canki-canka

# Wasan Canki-canka

## Kashi Na 1

### Tattaunawa a Aji

Rarraba Takardar darasin Wasan Canki-cankar sannan ka nemi kowane mahalarcin taron da ya cike ta. Nemi mahalarta taron da su zaɓi bayanai guda huɗu da za a raba sannan ka sanar da su cewa za ka raba bayanan da suka rubuta da ƙungiyar gaba ɗaya. Ba su umarnin cewa su ajiye takardar ta biyun.

Ba mahalarta taron mintuna 10 domin su kammala takardar darasin. Bayan nan, karɓi takardun darasin.

### Sanar da Ɗalibanka

Yanzu zan karanta wasu daga cikin bayanan da ke cikin kowace takardar darasin. Yi amfani da sashin Canki-cankar domin ka rubuta abun da kake hasashe game da wane mahalarcin taron ne zai cike kowace takardar darasin.

### Tattaunawa a Aji

Bayan ka karanta takardar karatun, sanya ƙungiyar a cikin tattaunawar.

### Tambayi Ɗalibanka

Shin akwai wani bayanin da ba ka raba ba shi da kowa ba? Waɗanne? Me yasa?

Shin kowa da kowa ya yi zaɓi iri ɗaya game da abun da za ka raba? Me yasa / me zai hana?

Ya danganci wanda za ka raba da shi, me yasa sa ka raba wasu irin wannan bayanan da yawa, ko kaɗan? Yaushe za ka raba shi?

Yaya sauƙin da aka samu wajen raba kowane bayanin da mutum ya rubuta / ya faɗe shi?

Shin akwai wasu misalai inda wata amsar da aka bayar ta isar da wani abu da gangan baya ga amsar da aka bayar ta ainihi (misali., ƙila wani ya riga ya bayyana abincinsa da ya fi so, wanda ya riga ya bayar da wasu alamu a kan al'adar da wannan mutumin ya waye da ita)?

Me kake tunanin wasu mutanen za su iya yin zato game da kai idan ka raba bayanin da ka rubuta a matsayin wani ɓangare na wasan canki-canka da mutanen duniya?

## Kashi Na 2

**Sanar da Ɗalibanka**

Sirri wata dama ce ta kula da abun da wasu mutanen suka sani game da kai. Za ka iya yin wannan ta hanyar faɗin wasu abubuwan game da kanka (kamar sanar da wasu mutanen adireshinka ko abun da kake son yi don nishaɗi) ko yin abubuwa a kewaye da wasu mutanen (kamar zuwa kanti tare da abokanka da kuma ɗaukar abin da ka fi so sosai). Sirrin na da tasiri ko kana cikin ɗaki tare da wasu mutanen ko kuma kana yin magana da su ta intanet.

Sirri ya danganci irin naka hukuncin da ka yanke ne. Abun da sirri ke nufi a gare ka da iyalinka zai iya bambanta a kan abun da sirri ke nufi ga wasu mutane a cikin wannan ƙungiyar da iyalansu. Idan muna da masaniya a kan abun da muke darajawa a matsayin sirri, da kuma yanda ɗabi'unmu a intanet za su iya tsara sirrinmu, za mu iya yin zaɓin da ya dace game da wane irin nau'in sirri muke so.

Haka kuma sirri yana canzawa dangane da nau'in bayanin da aka raba da kuma wanda aka raba da shi.

**Tambayi Ɗalibanka**

Misali, shin za ka raba adireshin gidanka da waɗannan mutanen:

1. Iyayenka / masu ba ka kulawa ko wasu manyan mutane a cikin iyalinka?

2. Abokanka?

3. Malaminka?

4. Baƙo / wani mutumin da ba ka sani ba sosai?

5. Wani abokin aboki?

6. Wata ƙungiya ko kamfani?

# Taƙaitawa

**Sanar da Ɗalibanka**

A lokacin da ka raba bayani a intanet, yana da muhimmanci ka yi la'aƙari da wanda zai iya ganin wannan bayanin sannan kuma kai ko mutumin da aka raba bayaninsa zai samu natsuwa dangane da raba wannan bayanin tare da wasu masu sauraron.

Wasu bayanan za su iya nufin abubuwa marasa daɗi a nan gaba idan aka raba su da mutanen da ba daidai ba. Idan baƙo / mitumin da ba ka sani ba da kyau ya san wurin da kake zaune, za su iya zuwa gidanka, wanda zai iya zama babu tsaro. A yayin da wannan zai iya yawaita ko kuma ƙaranta a wasu ɓangarorin duniyar daban-

daban, haɗarin (da kuma mummunan lahani) zai iya ƙaranta yiwuwar cewa zai iya faruwa. Domin gano zaɓuɓɓukan sirrin da za su kare lafiyarka, kana buƙatar ka fahimci abubuwan da sakamakon raba bayanin zai haifar.

# Rashin fahimtar magana

## Tattaunawa

**Sanar da Ɗalibanka**

Bari mu yi magana a kan abin da muke faɗi a cikin saƙonnin kar ta kwana, yanda muke faɗi, da kuma yanda zai iya bambanta da yin magana baki da baki.

**Tambayi Ɗalibanka**

Ta yaya faɗin wani abu a saƙon kar ta kwana zai iya bambanta daga faɗin shi baki da baki?

1. Idan ba ka ganin martanin da mutumin ya yi, ba za ka iya sanin abun da suke ji game da abin da ka faɗa ba. Za ka iya ɓata ma wani rai ba tare da ka sani ba.

**Sanar da Ɗalibanka**

A lokacin da ake magana da wani baki da baki, za ka iya lura da martaninsu a lokacin da ka yi magana da su, har da motsa jiki da kuma murya. Ana rasa wasu abubuwan a lokacin da ake magana ta intanet.

Duk da haka, za ka iya samun wasu nau'o'in bayanan ta intanet da za su iya taimaka maka wajen sadarwa (misali., dandalin sadarwar zamanin za su iya kasancewa suna da wasu ƙayyadaddun ƙa'idoji da za su samar maka da fahimtar da ta dace dangane da yanda ake fayyace bayani).

**Tambayi Ɗalibanka**

Idan ba ka da wasu alamomin da za su taimaka a fahimta (misali., nuna alama da jiki, murya), ta yaya wannan zai iya kaiwa ga a yi ma saƙonninka ko saƙonnin kar ta kwananka mummunar fahimta ta intanet daga wurin waɗanda za su samu saƙon (misali., ana iya yi ma wata maganar wasan mummunar fahimta sannan ta cutar da wani)?

Idan an yi ma firar da kake yi baki da baki mummunar fahimta, me za ka yi domin ka kau da wannan mummunar fahimtar (misali., za ka iya bayar da haƙuri ko kuma ka yi bayani a kan abin da kake ƙoƙarin faɗi)? Ta yaya wannan zai bambanta (ma'ana., wahala ko saƙi) da saƙon kar ta kwana?

# Wane ne mai sauraronka?

## Kashi Na 1

**Sanar da Ɗalibanka**

A yayin da ba za mu iya barin bayanin gwaji daga ayyukanmu na intanet ya faru ba, akwai wasu hanyoyin da za mu iya kula da sirrinmu da kuma kula da mutuncinmu a intanet. A cikin bayanan dandalin sadarwar zamani, akwai wasu saituna da aka sanya su a cikin dandalin da suke ba mu damar zaɓar wanda zai iya ganin abun da muka aike da shi. Ko da yake gyra waɗannan saitunan ba ya ƙayyade nazaris — ciki hare da nazarin metadata — daga, misali, wasu (misali., masu talla, masu bincike, ko kamfanoni) da kuma dandalin sada zaumuntar su kansu, haka kuma za su iya ƙayyade wasu abubuwan da masu amfani da dandalin sadarwar zamani za su iya gani ko wasu bayanai ne kamfanoni ko masu talla za su iya shiga cikinsu.

Ga waɗanda suka zaƙa, metadata wani bayani ne game da bayani. Metadata zai iya haɗawa har da, amma ba a ƙayyade su ga, abubuwa kamar wane lokaci ne ka shiga cikin dandalin sadarwar zamani, wurin da kake a lokacin da shiga ciki, da bayani game da mutanen da ka haɗu da su ta intanet.

Saitunan sirri za su iya bambanta a kan kowane dandalin sadarwar zamani, amma suna taimaka mana wajen bayani a kan masu sauraronmu. Misali, saitunan za su iya bayar da dama ga aikenmu domin su kasance na kowa da kowa gaba ɗaya, abokan abokai ne kawai za su iya gani, ƙayyadaddun ga aboki ɗaya kawai, kuma, wani lokacin, wasu zaɓaɓɓun abokai ne kawai za su gani. Sauran nau'o'in ayyukan da waɗannan saitunan za su iya yin tasiri a kai sun haɗa da bayanin wuri da kuma izinin rabawa. Cookies, tallace-tallacen da ake nufi, da kammala bincike za a iya kashe su duka a kan ayyukan da yawa ta hanyar wasu canje-canje a cikin zaɓuɓɓuka / saituna a kan kowane aiki. Haka kuma akwai ƙarin burauzar shafin yanar gizo da sauran ayyukan da ake da su iya tsawaita kariyar sirrinka a lokacin da kake matsawa a tsakanin shafukan yanar gizo (misali., Privacy Badger “Kar A Bi Sawu” ƙari daga Electronic Frontier Foundation).

## Kashi Na 2

**Tattaunawa a Aji**

Raba mahalarta taro bibbiyu

**Tambayi Ɗalibanka**

Ɗauki minti guda domin ka yi tunani game da dandalin sadarwar zamani duka inda kowannen ku ke da asusu.

Shin kasan abun da saitunan sirrinka na yanzu ke ciki a kan kowane ɗaya daga cikin

waɗannan dandalin sadarwar zamanin?

# Ayyukan Ƙungiya

### Sanar da Ɗalibanka

Bari mu bincika abubuwan da waɗannan saitunan suka samar sannan mu fito da waɗanda suka fi dacewa, a kowane yanayi, sannan kuma a kan wane dandalin.

Ɗaya bayan ɗaya, tafi dandalin sadarwar zamanin da kake yin amfani da shi sannan ka bincika saitunan sirrinka. Yawanci, za a iya samun saitunan sirrin a ƙarƙashin saitunan asusunka, da kuma wasu dandalin da suke da wasu ayyuka na musamman a kan bincika saitunanka.

Bayan ka bincika saitunanka, yi magana da abokin hulɗarka game da waɗannan saitunan. Me yasa kowannen ku ke da saitunan sirrinsa ta hanyar da yake da shi? Shin a wasu lokutan saitunan sirrin a cikin rubutu suke (misali., wasu saitunan sun dace ne a wani yanayin amma ba su da muhimmanci a wani)? Shin ka taɓa canza saitunanka? Ta yaya kake canza su kuma me yasa?

Ka tabbata kana kallon saitunan sirrin guda biyu waɗanda suka danganci raba bayani da mutane mabambanta a kan dandalin, da kuma waɗanda suka bayyana yawan bayanin da shi kansa dandalin da kuma duk wani wanda aka danganta shi da shi (kamar masu talla) za su iya samu. Dukkansu wasu ɓangarori ne na kula da sirrin bayani ga baƙi / mutanen da ba ka sani ba sosai, abokai, da kamfanoni.

### Tattaunawa a Aji

Ba mahalarta taron mintuna 5 domin su tattauna batutuwan sannan a shigo da ƙungiyar gaba ɗaya a cikin tattaunawar ta hanyar yin amfani da waɗannan tambayoyin.

# Tattaunawa

### Tambayi Ɗalibanka

Shin an saita asusunka gaba ɗaya zuwa na kowa da kowa, na sirri, ko wani abun daban? Yaya ka yanke shawara a kan wannan saitin?

Shin saitunan sirrinka na yanzu sun kasance yanda kake son su?

Yaushe ne yafi dacewa a raba abubuwa da kowa da kowa, kuma yaushe ne za a fi son saitunan sirri?

Shin kana samun natsuwa wajen raba bayananka tare da dandalin sadarwar zamanin da kake yin amfani da su ko kuma kamfanonin da ke yin tallace-tallace a

waɗannan dandalin? Mene ne ko kuma me zai hana?

Shin wannan tattaunawar ta sanya ka yin tunani danan game da saitunan sirrinka? Mene ne ko kuma me zai hana?

# Aiki

## Aiki

### Aiki

Yanzu da muka yi magana game da sirri, abin da mutane za su iya rusawa bisa ga abubuwan da muke rabawa, bambancin yanda mutane daban-daban za su fahimci saƙonni, da kuma dalilin da zai sa saituna su taimaka a matsayin wani kayan aikin da za ka so ka raba tare da wani mai sauraron, bari mu sanya abubuwan da ka koya a aikace.

A cikin mintuna 30 na gaba, ɗaya bayan ɗaya, nuna a kan waɗannan labaran guda uku sannan ka rubuta amsa a wani ɗan gajeren sakin layi ga kowanne:

1. Sinead ʻyar shekaru goma sha uku ce, kuma yanzu ta fara shiga harkar waƙa. Tana jin cewa ba ta zama hamshaƙiya ba tukuna, amma tana so ta raba wani sabon salo tare da abokanta kuma ta samu taimakon da za su bayar a kai. Tana yin la'aƙari da ƙara wasu bidiyoyi na waƙoƙinta daga cikin waƙoƙin da ta fi so a kan dandalin sadarwar zamani. Wane irin dandalin sadarwar zamani ne za ka bayar da shawara? Mene ne kake ganin zai iya zama saitunan sirrin ainihi na wannan dandalin? Ka ɗan yi bayani a kan dalilin.

2. Raza ɗan shekaru goma sha shida ne, kuma yana da sha’awar girki da ƙirƙiro sababbin girke-girke. Ya yi girki da yawa a kan abinci mai ɗauke da naman kaza kuma yana matuƙar farin ciki da hakan, sannan yana so ya raba girke-girken da abokansa da sauran mutanen da ke sha’awar girke-girke. Wane irin dandalin sadarwar zamani ne za ka bayar da shawara? Mene ne kake ganin zai iya zama saitunan sirrin ainihi na wannan dandalin? Ka ɗan yi bayani a kan dalilin.

3. Ulwazi ʻyar shekaru goma sha takwas ce, kuma tana so ta fara neman aiki a wata mai zuwa. Ta san cewa masu ɗaukar aiki suna so su ga taƙaitaccen tarihin karatu, amma ba ta da tabbaci a kan yanda ake rubutawa. Tana sha’awar yin aiki a sashin Kimiyyar Kwamfuta, amma ba ta san wasu ayyuka ba ne za ta iya samu kuma ko ta cancanci samun waɗannan matsayin. Tana so ta samu shawara ko shawarwari daga wurin wasu waɗanda suke sha’awar kwatankwacin wannan aikin, amma babu wani daga cikin abokanta da ke aiki sashin Kimiyyar Kwamfuta. Wane irin dandalin sadarwar zamani ne za ka ba Ulwazi shawara a kai? Mene ne kake ganin zai iya zama saitunan sirrin ainihi na wannan dandalin? Ka ɗan yi bayani a kan dalilin.

Idan zai yiwu, a lokaci na gaba da kuka sake haɗuwa a matsayin ƙungiya, raba mahalarta taron bibbiyu, sannan ka ba kowace ƙungiyar mutum biyu damar raba aikinsu.

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.